
# MAGAMA

Agusta/Satumba 2005 Shaaban 1426 Kyauta



Jigon Wallafa:


- Amirkawa Na Tsoron Allah
- Kwallon Kwando Ya Shahara
- Tunawa Da Ta'addancin Satumba 11

A Cikin:

- Kokarin Kai Wa Matalauta Tallafi
- Musayar Al'adu
- Amirka Na Goyon Bayan Sake Tsarin Harkokin Iskar Gas

## "Amirka Na Kare 'Yancin Musulmi" - Imam Fu'ad

ISSN 0794-0262




PRESIDENTIAL EMERGENCY PLAN FOR AIDS RELIEF
UNITED STATES MISSION IN NIGERIA

girl child art foundation
A NON GOVERNMENTAL ORGANIZATION FOR THE GIRL CHILD
No 1 Bisi Anagbogu Lane Off Amaenyi GSS, Awka, Anambra State.
Tel: 08033486429, 048551264, e-mail: girlchild@gcafy.org, adaonyejike@yahoo.com. URL: www.gcafy.org.

MAGAMA

Satumba 2005 Jimada Akhir 1426 Kundi Na 1, Fitowa Ta 19



A wannan gabatarwar Mujallar *Magama,* duk hankalina ya koma ne ga waɗanda bala'in guguwar Katrina ya yi wa ta'adi, da kuma mummunar ɓarnar a yammacin bakin gaɓar teku da ke yankunan Alabama da Louisiana da kuma Mississippi.

An bayyana cewa guguwar ta Katrina ta fi dukan munanan haɗurran guguwa goma da aka taɓa samu a tarihin Kasar Amirka muni, kuma Amirka ba ta taɓa kiɗimewar yunƙurin neman samun agaji da aikin ceton rayukan jama'a, a ƙasar ba, irin wannan lokacin. Amma ba abin mamaki ba ne, domin jihohin uku, masu faɗin murabba'in mil dubu 90, da wannan guguwar, ta abka wa, sun kai ko ma sun fi faɗin nahiyar Kasar Ingila. Kamar kuma yadda aka gani a kafofin telebijin, irin asarar rayuka da dukiyoyin da aka yi, sun fi ƙarfin misaltuwa. Fiye da mutane 700 suka rasa rayukansu, yayin da aka kwashe ɗimbin jama'a zuwa jihohi 15 da yankin Columbia.

Amma abin mamaki, kai-tsaye za a iya cewa irin ɗimbin taimakon da ƙasashen duniya suka bayar, wani al'amari ne da ya bai wa Amirkawa mamaki. Kasashe 117 da ƙungiyoyi na duniya 12 suka bayar da agajin kuɗaɗe da kayan shimfiɗa da na'urorin aikin ceto.

Ita kanta, Hukumar Gaggauta Bayar da Agaji ta Amirka (FEMA) ta samu zunzurutun kuɗi fiye da dalar Amirka miliyan 460 daga ƙasashen duniya, cikinsu kuwa har da Kasar Namibia da ta bayar da kayan agaji na dalar Amirka dubu 100 da tsabar kuɗi dalar Amirka, dubu 50, daga Djibouti. Ofisoshin jakadancinmu 20 da ke Afirka, cikinsu kuwa har da Ofishin Jakadancin Amirka a Nijeriya sun karɓi saƙonnin jaje fiye da dubu 22. Abin alfahari ne kuma, irin yadda ɗimbin 'yan Nijeriya suka riƙa bayar da taimako. Ɗaya daga cikin irin waɗanan taimakon shi ne wanda wani bawan Allah, wanda ko Amirka bai taɓa zuwa ba, amma saboda tausaya wa irin abin da ya gani a telebijin, ya bayar. Haka ma wata ƙungiyar ci gaban ƙasashen duniya ta rukunin Kolejojin baƙaƙen da ke Yankin Mississippi (MCID) da ke hulɗa da gwamnonin jihohi 13 da kuma majalisun dokokin jihohin Nijeriya, ta shirya da Bankin Standard Chartered Bank, da ke Abuja, da ya karɓi duk wani taimakon kuɗin Amirka ko na Nijeriya, don agaza wa waɗanda Bala'in na Guguwar Katrina ta abka wa.

Wata ma ƙungiyar, mai zaman kanta mai suna Kungiyar Kula da Muhalli ta Afirka (EANET Africa) da ke Nijeriya, ta fara irin wannan shirin da Bankin ECO Bank. A halin yanzu ma, Shugaba Bush da Sakatariyarsa Rice da Jakada Campbell, suna matuƙar alfahari da irin karimci ta goyon bayan da ƙasashen duniya suka bayar, musamman, Nijeriya.

Yanzu kuma bari in gutsuro wa masu karatu kaɗan daga cikin irin abubuwan da wannan fitowar ta ƙunsa. Mafi yawan labarun sun ƙara feɗe biri har wutsiya ne game da abubuwan da suka jiɓinci jama'a. Kanun labarinmu dai game da Liman Fu'ad Adeyemi ne, dangane da yadda ya kutsa kan gano irin yadda ƙungiyoyin Islama suke a Amirka. Mun kuma kawo muku labarin wata ziyarar musamman da tsohon shugaban Amirka, Jimmy Carter da uwargidansa suka duƙufa a kai, don ci gaba da irin taimakon da suke bayarwa dangane da ayyukan magance cutar Kurkunu da Dundumi, a nan Nijeriya.

Bayan shekaru 16 da suka yi suna fafatawa, Shugaba Carter da takwarorinsa na Nijeriya, cikinsu har da Ministan Lafiya da Janar Yakubu Gowon, sun lashi takobin kawar da cutar kurkunu a Nijeriya, nan da shekaru biyu masu zuwa, watau 2007. Haka ma, wani shahararren jarumin fina-finai, Wesley Snipes, ya kawo ziyara Nijeriya, domin ƙara jadadda muhimmancin harkokin yawon shaƙatawa, a Nijeriya, musamman saboda jama'ar Afirka da ke zaune a sauran ƙasashen duniya. Su kuma Musulmin da za su yi azumin watan Ramadan, a cikin watan Oktoba, ina fatan Allah ya karɓi ibadarsu, aikin kuma ya zama darasi a garemu.

*Claudia E. Anyaso*

MA'AIKATAN MUJALLA

CLAUDIA E. ANYASO
Jami'ar Hulɗa Da Jama'a A Nijeriya

RUDOLPH E. STEWART
Jam'in Labarai

SANI MOHAMMED
Edita

ISHAKA ALIYU
Mai Ba Da Shawara Game Da Wallafawa

Ofishin Jakadancin Amirka ke wallafa wannan mujallar kowane wata. A aiko da wasiƙu zuwa ga
Sashen Hulɗa da Jama'a, Lamba 1075 Titin Difulomasiyya, Tsakiyyar Gari, akwatin gidan waya mai lamba: 5760, Abuja, Nijeriya.
09-4614000 Fax: 09-4614011. Ofishin na Legas: akwatin gidan waya mai lamba: 554, Legas.
Tel: 01-2632577, 2633560, 2633395. Na'urar INTERNET: http://nigeria.usembassy.gov/wwwhmagama.html

# "Amirka Na Kare 'Yancin Musulmi"

## – *Liman Fu'ad Adeyemi*

Daga Sani Mohammed
*Editan Mujallar Magama*

Ustaz Fu'ad Adeyemi sanannen malamin Islama ne, kuma limami, wanda ke kula da ɗaya daga cikin manyan ƙungiyoyin da ke yaɗa da'awar addinin Islama, a Babban Birnin Tarayya da ke Abuja, watau Kungyar Al-Habibiyya. Liman Adeyemi na ɗaya daga cikin waɗanda suka halarci wani shiri da Gwamnatin Amirka ta shirya don shugabannin ƙungiyoyi daga ƙasashen duniya, a kan "Harkokin Addini da Kyautata Rayuwar Jama'a". Ya ce da farko na yi watsi da gayyatar da ma'aikacin Sashen Harkokin Al'adu na Ofishin Jakadancin Amirka ya yi mini, har sai da ta kai na muzguna masa, domin ina matuƙar ƙyamar Kasar Amirka, saboda irin labarun da nake ji game da ita. Amma saboda irin ban bakin da abokansa da 'yan uwansa suka riƙa ba shi, ya kuma yi koyi da hadisin Annabi Muhammadu (Tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi), dangane da niƙar gari zuwa ko'ina domin ƙaro ilimi, sai Ustaz Adeyemi ya amince da ya amsa gayyatar zuwa Amirka. A cikin wata 'yar gajeruwar hirar da suka yi da Editan Mujallar Magama, Sani Mohammed, Ustaz Adeyemi ya tuna da irin faɗakarwar da ya samu, da kuma yadda ta wanke dukan irin ƙyamar da yake yi wa Amirka.

<u>Tarihi:</u>

An haifi Ustaz Fu'ad Adeyemi, ranar takwas ga watan Yuni na 1966, a garin Odeomu na Jihar Oshun. Kuma ya fito ne daga gidan malamai, amma da farko Ustaz Adeyemi bai da niyyar gadon kakanninsa dangane da zama malamin addini, ko kuma limami, duk da yake ya fito ne daga wani tsatso na shugabanni da malaman addinin Islama, har da kakan-kakansa da ya fito daga Gwandu ya zo ci rani a Odeomu, inda yau Ustaz Adeyemi ke tinƙahon mahaifarsa ce.



Malam Fu'ad Adeyemi shi ne babban Limami na Masallacin Al-Habibiyya da ke Abuja.

A duk lokacin da Ustaz Adeyemi ke ƙara guje wa zama mai wa'azin addinin Islama, bai sani ba sai ya yi ta ƙara shiga cikin gawurtattun malamai. Kuma irin sha'awarsa ta ƙara samun ilimi ya kai shi Jami'ar Badun, inda ya samu digirinsa na farko a fannin Addinin Islama, a 1972. Daga nan kuma ya bauta wa ƙasa a Cibiyar Horar da Addinin Islama, a Madalla, wanda har ya samu muƙamin gudanar da harkokin

Duba Shafi Na 4

# Amirkawa Na Tsoron Allah *"Ni Kam Na Ga Gaskiya"* *- In Ji Abdul Carimo Sau, Musulmi Ɗan Kasar Mozambik*

Daga
Jim Fisher-Thompson da Gregg Garland
*daga Washington*

Wani ɗan Kasar Mozambik Musulmi, Abdul Carimo Sau, ya bayyana cewa duk ja-game da raɗe-raɗin da ake yi game da Amirka yanzu ya kau, lokacin da ya share makonnin uku yana zagaya Kasar Amirka, a inda ya riƙa tarurruka da Amirkawa a ƙananan garuruwa, wanda abin da ya ba shi mamaki shi ne yadda idanunsa suka buɗe ya fahimci cewa Amirkawa suna addini.

Sau, wanda shi ne Mataimakin Shugaban Majalisar Musulmi ta Kasar Mozambik, ya halarci wani shiri ne da Amirka ta shirya wa shugabannin addinai da jama'a na ƙasashen duniya, wanda Sashen Ilimi da Al'adu na Amirka ya ɗauki nauyin gudanarwa.

Lokacin da ya dawo gida, Sau ya zanta game da tafiyarsa, a shirin wani ƙaramin gidan redio na Musulmi, mai suna *TalkShow* ranar 22 ga watan Agusta. Bayan kwanaki biyu kuma, tare da haɗin gwiwar Ofishin Jakadancin Amirka, Malam Sau, ya kira wani taron tattaunawa da shugabanni Musulmi da kuma ɗalibai Musulmi game da hirar tasa a rediyo.

A cewar wata ƙasidar da Ofishin Jakadancin Amirka da ke Birnin Moputo ya bayar, Malam Sau ya "buɗe zuciyarsa" game da wannan taron da ya halarta, inda ya bayyana cewa "na gane wa idanuna ƙasa mai ɗimbin addini, da yawan jama'a daban-dabam, kuma suna girmama addininka, ba tare da sanin al'adunka ko ɗabi'unka ba."

Wani abin da ya soka game da jama'ar ta Amirka shi ne cewa irin hada-hadar da suka saba yi, ba za su iya jure wa irin lokuttan da ake sharewa ba, lokuttan tarurruka da cin abinci, irin na Afirka. Shi abin da ya so a riƙa ɗaukar lokaci wajen zantawa, in ji shi.

A lokacin hirar rediyon, wadda aka sanya har tsawon fiye da awa ɗaya, Sau ya jaddada irin yadda Amirkawa ke da tsoron Allah, da kuma yadda Musulunci ke bunƙasa a Amirka.

Ya ce, a farko farko da ya kai ziyara Amirka, ya gane cewa Amirkawa dabam suke daga dukan irin ja-game da raɗe-raɗin da ake yi game da su, a gidajen watsa labarai. A gaskiya, Musulunci ya haɓaka a Amirka, ba don komai ba, sai don gwamnati na nata ne, masu addini na nasu, wanda ya nuna cewa, kowa na da 'yancin walwala da addini, a wannan ƙasar mai ɗimbin bambancin ra'ayi da aƙida da sai Musulmi za su ci amfaninsa. Da yake amsa wata tambaya, Sau ya ji takaicin yadda Musulmi a Mozambik ke shakkun sa hijabi ko rawani, a bainar jama'a, yayin da babu ruwan Amirkawa da wannan, wurin da ake girmama ka da addininka.

A wajen wannan taron na ranar 24 ga watan Agusta, shugabanni Musulmi daga ƙasashe 40 ne da kuma waɗansu ɗalibai Musulmi, 'yan ƙalilan suka halarci taron.

Bugu da ƙari, Sau ya yi magana sosai game da ziyarar tasa, inda ya fi yin bayani game da addinin Amirkawa, da lokuttan da suka zauna don cin abinci da kuma irin karimcin da aka nuna masu, in ji shi. Ya ce babban abin da addini ya yi a Amirka shi ne, tallafa wa harkokin jin daɗin rayuwa, ta kowane fanni, a inda ya yi nuni da misalin "Father Joe", Carroll na Birnin San Diego. (Carroll limamin katolika ne, da ke da wata makekiyar tsangaya domin bai wa marasa galihu muhalli). Ɗan Kasar ta Mozambik ya ce Amirkawa sun ba shi mamaki, musamman yadda suke kyautata jin ƙai ga gajiyayyu. Da aka tambaye shi game da Musulunci a Amirka, Sau, ya nuna cewa, duk wani ɗan gari za ka samu masallaci, kuma, ba kamar yadda 'Yan Jarida ke faɗa ba, Musulmi sun fi su yawa nesa ba kusa ba. Ya ce har rawani ya yi, ko don wani ya yi magana, amma sai ya ga babu wanda ya ce masa kanzil. Sai ma ya lura cewa irin al'amuran da ke fuskantar Musulumi a sauran ƙasashen duniya, ba su faruwa a Amirka. Da ya juyo kan harkokin siyasa, Sau ya yi tsokaci ne game da tsoma bakin Amirka a Gabas Ta Tsakiya.

Ya kuma jaddada cewa, Falasɗinawa da Yahudawa, sun fi amince wa Amirka ta shiga tsakaninsu, fiye da kowa.

Game da yaƙin Iraƙi kuma ya faɗa wa masu sauraron sa cewa Amirkawa ba 'yan amshin Shata ba ne. A halin yanzu ma, kullum sai tabka muhawara ake yi game da yaƙin na Iraƙi a majalisu da gidajen watsa labarai. ■

# Amirka Na Kare 'Yancin Musulmi

Daga Shafi Na 2
cibiyar, kafin ya koma Cibiyar Harkokin Islama ta Shehu Shagari da ke Garki, ta Birnin Abuja. Daga nan sai gaskiya ta fara halinta, ya zama limamin farko na Masallacin Ansar-Udeen da ke Abuja. A kuma cikin watan Disamba na 2002 ne, Ustaz Adeyemi ya bar Masallacin na Ansar-Udeen, domin kafa wannan cibiyar ta yaɗa Da'awar Addinin Islama, da ake kira Al-Habibiyya. Ya kuma shahara a kan irin huɗubar da yake yi, mai ratsa zukata, a lokacin sallar Jumma'a, wadda kuma ita ta janyo hankulan masallata ga zuwa Masallacin na Al-Habibiyya.

Ga yadda hirar ta kasance:

Magama: Wane irin tunani kake da shi game da Amirka, kafin wannan ziyara, kuma ya ya ka ji, lokacin da aka gayyace ka da ka halarci wannan taron na ƙasashen duniya game da "Harkokin Addini da Kyautata Rayuwar Jama'a"?

Ustaz Adeyemi: Kafin in je Amirka, ba ni ƙaunar ta ko ƙwayar zarra. A gaskiya, ba ni ƙaunar wata alaƙa ta haɗa ni da duk wani ma da ke da dangantaka da Amirka, duk da yake na sha saduwa da Amirkawa na kuma taɓa halartar wani shirin da ofishin Jakadancinta ya shirya wa Kungiyar Makaɗa Musulmi da ake kira "Native Deen", lokacin da suka ziyarci Abuja. Lokacin kuma da aka dumfare ni da in cika waɗansu takardu wai don halartar wannan taron, na faɗa wa jami'in da ya aiko mini da takardun cewa ban da sha'awa. Kai har musguna masa na yi. Na kuma watsar da takardun ne, har yara na suka riƙa hidima a kansu. A gaskiya, kafin in je Amirka, ban san wata ƙasa da na ke gani ta fi ta zalunci ba. Ina ganen ta kamar ƙasar da ke jin daɗin hallaka rayukan jama'a. In tsage maka gaskiya, ba ni ƙaunar dukan mahalukin da ba ya son addinina na Islama. Amma abokaina da 'yan uwana ne suka shawo kaina ga zuwa Amirka, ciki kuwa har da matata, wadda ta ba ni shawarar da in gwada. Na je Amirka ne, domin ganin ƙwaƙwaf, sai ga shi ziyarar ta amfane ni. Lokacin da na bar Abuja zuwa Amirka, na riga na sadaƙar da dukan abin da zai faru, musamman tun lokacin da Ofishin Amirka, da ke Legas, ya ƙi amince mini da shaidar iznin shiga ƙasar. Wannan shi ya sa na fara waswasin zuwa Legas, lokacin da Ofishin Karamin Jakadancin ya gayyace ni. A nan na cewa kaina wataƙila waɗannan Amirkawan suna son yin amfani da wannan damar ne, domin halaka ni. Na kuma tabbatar suna sane da irin yadda nake zafafa wa'azina da kuma irin rashin ƙaunar da nake nuna wa ƙasarsu. Na ɗan tsorata, amma sai na yi tawakkali, domin duk wani Musulmi ya san babu wanda ya isa ya yi masa wani abu, sai Allah Ya yarda. Abin



Liman Fu'ad Adeyemi ne nan yake hira da 'yan jaridu. Tare da shi, akwai Dr. Rudolph E. Stewart, Jami'in Watsa Labarai na Ofishin Jakadancin Amirka da kuma Mrs. Shirley Lisenby, Jami'ar Kula da Harkokin Al'adu a Sashen Hulɗa da Jama'a.

mamaki, lokacin da na isa ofishin ƙaramin jakadancin, Jami'in biza, Mista Howe, sai ya yi mini kyakkyawar marabar da har godiya na yi masa. Ina kuma godiya ga Mista Bath Suwa, game da irin juriyar da ya yi har ya fahimce ni.

Magama: Waɗanne irin abubuwa ka gani, kuma mene ne ra'ayinka game da Amirka a yanzu?

Ustaz Adeyemi: Na fahimci halin jama'ar Amirka game da jin ƙai da kuma bambancin ra'ayoyinsu a kan manufofin gwamnatinsu. Na yi ta faɗar haka a tarurruka da dama da na yi da manyan jami'an gwamnatin Amirka a Birnin Washington. Na faɗa masu cewa, a dalilin wannan ziyarar, na fahimci cewa akwai matuƙar bambancin ra'ayoyi, a tsakanin halayyar jama'ar Amirka ga Musulmi da kuma ra'ayoyin gwamnati da suka jiɓinci harkokin sauran ƙasashen duniya. Na fahimci cewa Amirkawa na tsoron Ubangiji a kan duk abin da za su yi, kuma suna matuƙar ƙaunar ƙasarsu, duk da bambancin irin addinan da suke bi. Na kuma fahimci cewa duk da yake Nijeriya tana da bambancin jama'a, dukan ƙabilun da ke zaune ƙasar suna da wani abu ɗaya da yake sa su zama da juna amma a ɓangaren Amirka, akwai ƙabilu da addinai da dama da babu ruwansu da juna, amma duk da haka jama'a na zaman lafiya. Wannan na ɗaya daga cikin irin abubuwan da nake fatan 'yan Nijeriya za su yi koyi da shi.

Magama: Me ka fahimta, kuma ta yaya za ka yi amfani da abin da ka fahimtar?

Ustaz Adeyemi: Ya kamata shugabannin Nijeriya su yi koyi da halayyar Amirkawa, wajen girmama



Malam Fu'ad Adeyemi

ƙasarsu fiye da komai, duk da irin bambancin da ke tsakaninmu. Ya kamata mu ilmantar da jama'a. Ba ma jama'ar kaɗai ba, muna bukatar mu riƙa ilmantar da masu ilimi. A nan ina nufin masu wa'azi. Ya kamata mu zama masu tsoron Allah. Mafi yawan masu wa'azi ba su san Allah ba. Domin idan da sun san Allah, babu yadda za a yi su riƙa tunzura jama'a ga tayar da tarzoma, sai dai idan suna yi ne domin su azurta ko kuma su yi suna. Ko da yake akwai bambanci tsakanin harkokin gwamnati da na addini, amma jama'ar Amirka na gudanar da harkokinsu na addini, kuma gwamnati na ba su kariya, a ƙarƙashin Tsarin Mulki. Yanzu ra'ayina ya canza game da yadda na ɗauke ta. Amirka da na gani, musamman garin Charlotte na arewacin Yankin Carolina, ya sha bamban da irin abubuwan da ake yi a finafinan Hollywood. Kana iya bambance tsakanin ra'ayoyin gwamnati da na jama'a, domin ba kamar ra'ayoyin gwamnati ga ƙasashen duniya ba, jama'ar Amirka suna marhabin da sauran mutane da addinansu. A 'yar hulɗar da na yi da jama'a, na gano cewa suna ƙaunar Musulmi, inda matsalar take ita ce game da 'yan ta'adda, waɗanda suka yi imani da a ruguza komai. Musulmi na ta ƙoƙarin ganin sun faɗakar da jama'a game da bambancin Musulunci da kuma aikin 'yan ta'adda. A inda kawai na ga akwai matsala shi ne a filin jirgin sama, domin ba a taɓa yarda da ƙai, da zarar an ga cewa kana da sunan Musulunci. Musulunci na da ƙarfi a Amirka, kuma Musulmi sai ƙara yawa suke yi. Kuma na fahimci cewa, Musulunci ya fi kowane addini haɓaka, zahiran, a Amirka. Wani kuma abin da na koya, wanda nake son yin amfani da shi a Cibiyar Al-Habibiyya da ke Abuja, shi ne ƙwazon Amirkawa wajen bayar da agaji. Da yardar Allah, a wannan watan na Azumin Ramadan, Cibiyar Al-Habibiyya za ta kafa Asusun Ajiye Kayayyakin Abincin Azumi, don taimaka wa ciyar da marasa galihu. Wannan shirin ya samo asali ne, daga ziyarar da na kai ga wata ƙungiyar agaji da ke Garin Salt Lake, mai suna "Rescue Mission", wadda ke kula da marasa muhalli da bayar da ayyukan yi ga marasa shi da kuma ciyar da jama'a. Na kuma sake ganin irin wannan shiri, lokacin da na kai ziyara ga Kauyen Father Joe, da ke San Diego, inda ake bayar da muhalli da abinci ga marasa galihu, da kuma horar da jama'a koyon sana'o'in hannu. Muna fata za mu buɗe wani shirin musayar ra'ayoyin addinai, da kuma roƙon jami'o'i su riƙa koyar da ɗalibai haƙuri da juna, ta hanyar musayar ra'ayoyi. Za mu kuma fara da Jami'ar Abuja, da zarar an gama azumi. Zan fara wannan aikin tare da haɗin gwiwar takwarorina daga Kaduna, waɗanda suka kai irin wannan ziyarar da na kai a Amirka. ■

# “Musulmi Mata A Amirka Suna Da Bakin Magana”

Daga Afzal Khan,
*Mai Bayar da Rahoto na Musamman daga Washington*



Musulmai Mata a Amirka.

An bayyana cewa Musulunci addini ne da ke bai wa mata damarsu, saɓanin irin fahimtar da kafofin watsa labarai ke yaɗawa na cewar Musulmi mata ba su damu da yadda ake nuna ma su bambanci ba, a bisa tafarkin addininsu, in ji, wata ƙungiyar Mata Musulmi da ke Amirka, a wani taron tattaunawa da aka yi.

Precious Rasheeda Muhammad, wata baƙar fata Musulma, kuma editar *Mujallar Musulunci a Amirka* ce ta ɓullo da wani taron tattauna al'amurra da aka yi a ranar 11 ga watan Agusta, a Birnin Washington. Ta ce ko wannan taron wata alama ce, mai nuna cewa mata Musulmi da ke Amirka suna da 'yanci. Ta ɗauko tarihin manyan mata musulmi, tun lokacin da aka saukar da Alƙur'ani mai Tsarki, shekaru dubu ɗaya da 400 da suka shuɗe. Ta ce waɗansunsu shugabanni ne na siyasa, yayin da waɗansu suka ja ɗamara, daidai da maza, a fagen yaƙi, in ji ta.

Muhammad ta ce 'Yar uwa, Clara Muhammad, matar Mujaddadin Addinin Islama a Amirka, Elijah Muhammad ce, ta fara kira ga ilmantar da Musulmi a Amirka, game da ɗabi'o'insu da al'adunsu. 'Yar uwa Clara ta kafa makarantu da dama, don ilmantar da Musulmi baƙaƙen fata tun farkon 1930.

Ita kuma Gihan El-Gindy, wata baƙar fata, haifaffar Kasar Misira, kuma Darektar Cibiyar Koyar da Al'adun Jama'a (TEC) da ke McLean ta Jihar Virginia, ta ce an ɗan so a kaucewa saƙonnin Annabi Muhammad (SAW) game da addinin Islama, shekaru dubu ɗaya da 400, idan aka kamanta yadda jama'ar ƙasashen Musulunci, ke fassara su da gudanar da su.

“Al'adun da ayyukan addinin Musulunci sun bambanta a ƙasashe, saboda al'adunsu na gargajiya da kuma dokokin da bil-Adama ke kafawa”, in ji El-Gindy. Ta ce rahotannin da kafofin watsa labarai ke yaɗawa a kan musguna wa mata, a ƙasashen musulmi, sun samo asali ne daga irin al'adun jama'ar ƙasa.

“Maganar cewa, a matsayina na mace musulma a Amirka, dole in bari a musguna mini, ba ta da wani tasiri. Ina da ikon in yi walwalar da nake so. Harkokina daban da na mijina, kuma muna zaman arziki”, in ji El-Gindy. Ta jaddada cewa, yana da muhimmanci musulmin Amirka su samu damar zaɓen abin da suke son yi, da tafarkin rayuwa, su kuma tsaya kafaɗa da kafaɗa da duk wani jinsin Amirkawa.

Ita kuma Ayesha Mustafa, ita ma wata baƙar fatar da ta musulunta kwanan nan, kuma editar wata jaridar Musulunci, da ke fitowa kowane mako, mai suna *(Azizah) Muslim Journal*, ta bayyana cewa irin labarun da ake bayarwa game da Musulunci, ya taimaka wa musulmin Amirka, da su samu muryar faɗa, daidai da kowa, a harkokin da suka shafi ƙungiyoyin Kasar Amirka. Ta ce, “abin da Muja-llar Azizah take yi mini, shi Mujallar Ebony ke yi wa baƙar fatar Amirka. Ita ce muryata”.

Mata Musulmi na Amirka ne, suka kafa *Mujallar Azizah,* da ke fitowa bayan watanni uku, a cikin 2000, a Birnin Atlanta. ■

TUNI

# Ta'addacin Satumba 11

Ranar Lahadin da ta wuce ne, jama'ar ƙasashen duniya suka tuna da ranar cika shekaru huɗu da 'yan ta'adda suka abka wa Amirka, a ranar 11 ga watan Satumba, inda aka yi juyayi da 'yan koke-koken takaici. Kasashe, da mabiya addinai da jama'a da dama da ke da bambancin al'adu, sun yi tir da wannan aiki na ta'addanci, inda aka kashe jama'a da dama na ƙasashen duniya, ciki har da jama'ar Nijeriya.

Babban Sakataren Ma'aikatar Harkokin Kasashen Wajen Nijeriya, Jakada Nkem Nwadibia-Anyawu tare da Jadaka John Campbell, suka aza furen kallo, a Dandalin Yar'adua da ke Abuja, Nijeriya, inda limamai, da shugabannin mujami'u suka yi addu'o'in tunawa da waɗanda suka rasa rayukansu, a haɗarin ta'addancin ranar 11 ga watan Satumba. Hasali ma, tsohon Shugaban Amirka, Mista Jimmy Carter da uwargidansa Rosalynn da kuma Jakada John Campbell, sun shuka itaciya, a harabar Ofishin Jakadancin Amirka, don tunawa da irin sadaukar da kan da waɗanda suka rasa rayukansu suka yi a haɗarin 11 ga watan Satumba.

Mista Carter da uwargidansa, sun gana da zaratan sojojin ofishin jakadancin, suka kuma yaba masu, a kan irin yadda suke sayar da rayukansu, don Amirka ■



Liman Fu'ad Adeyemi tare da Mrs. Claudia Anyaso, Shugabar Sashen Hulɗa da Jama'a a Ofishin Jakadancin Amirka da ke Abuja



Raberen Fada Raymond Hickey na ɗarikar Katolika.



Ambasada Nkem Nwadibia-Anyawu tare da Jakadan Amirka a Nijeriya John Campbell ne suke ajiye furanni a wani shiri na musamman domin martaba waɗanda suka rasa rayyukansu a hare-haren ta'addanci.





Tare da sojojin da ke tsaron Ofishin Jakadancin Amirka da ke a Abuja, Tsohon Shugaban Amirka Jimmy Carter ne nan da Uwargidansa Rosalynn suke ƙoƙarin shuka itaciya a harabar Ofishin Jakadancin Amirka.

"A wannan biƙin, ba wai kawai mu na tunawa da waɗanda suka mutu a ƙunar baƙin waƙe ta Satumba 11 ba ne, amma duk waɗanda suka mutu a dalillin ta'addanci a duk faɗin duniya," In ji Ambasada Campbell.

# Kokarin Kai Wa Matalauta Da Mabuƙata Tallafi A Afirka

Tsohon Shugaban Amirka, Jimmy Carter tare da uwargidansa Rosalynn, sun sake komowa Nijeriya, a cikin watan Satumba, don yin tarurruka da shugabannin Nijeriya da jami'an kiwon lafiya da kuma shugabannin ƙungiyoyin jama'a.

An yi waɗannan tarurrukan ne don ci gaba da irin ƙoƙarin da suke yi na tallafa wa jama'a dangane da kawar da illolin cutar kurkunu da sauran ƙwayoyin cutar da ke haddasa cutar ta kurkunu da ƙudan tsando da kuma cutar dundumi, kazalika da cututtukan da ke gallabar jama'ar Nijeriya, shekaru aru-aru da suka wuce.

A wani taron haɗin gwiwar da suka yi da Ministan Kiwon Lafiya, Farfesa Eyitayo Lambo, a Abuja, Shugaba Carter ya ce, irin taimakon agajin da yake gudanarwa, wata alama ce ta tunanin jama'ar Amirka, ga kai taimako ga dukan waɗanda ke bukata a faɗin duniya, duk da yake ita kanta Amirkar tana fama da mummunan bala'in ta'adin guguwar Katrina a New Orleans.

Ambasada John Campbel ya ce, "tun lokacin da ya kammala shugabanci, Carter da uwargidansa, suka rungumi harkokin ganowa da aiwatar da duk wata mafita, game da harkokin zaman lafiyar duniya da mulkin dimokuraɗiyya da shugabanci nagari, da harkokin kiwon lafiya da samar da matsuguni, waɗanda suka zama masifofin da suka game duniya". ■



Tsohon Shugaba Jimmy Carter tare da Ministan Kiwon Lafiya na Nijeriya, Farfesa Eyitayo Lambo.





Waɗanda ke fama da ciwon kurkunu a ƙauyen Dunkure da ke Arewacin Nijeriya.



Daga dama: Tsohon Shugaban Nijeriya, Janar Yakubu Gowon, da Ministan Kiwon Lafiya na Nijeriya, Farfesa Eyitayo Lambo, sai kuma Tsohon Shugaban Amirka, Jimmy Carter. Daga hagu: Ambasada John Campbell da Uwargida Rosalynn Carter.

# Sa Hannun Jama'a Ga Kyautata Shirin Ilimin Firamare Ba Karamar Fa'ida Ba Ce *– Mis Suemo*

Daga
Sani Mohammed,
*Editan MAGAMA*

Watakila abin da ya fi ɗauke wa iyayen yaran Nijeriya hankali yanzu, bai wuce tunanin ingancin ilimin da yaransu ke samu ba, musamman a makarantun gwamnati a wannan lokacin da ake ƙoƙarin komawa makarantu, a cikin watan Satumbar nan. Yanzu a ƙasar ana nan ana ta tabka muhawara, asali ma, a dukan ƙasashen duniya, a kan bukatar da ke akwai ta hanyar sanin yadda za a fuskanci kyautata ɓangarorin ilimi. Masana da dama sun yi imanin cewa irin koma-bayan da ake samu ga ingancin ilimin ɗaliban da ke zuwa jami'o'in Nijeriya, ya samo asali ne daga taɓarɓarewar yadda ake koyar da ilimi a makarantun firamare da sakandare.

A sakamakon wannan muhawarar ne, kwanan nan, Ofishin Jakadancin Amirka a Nijeriya, ya zaɓo Babbar Jami'ar Ilimi a Hukumar Ilimi ta Babbar Birnin Tarayya, Mis Ashirshima Suemo, don halartar wani taron shirin harkokin ilimi, na yankunan duniya, da aka shirya, a kan "Al'amurran Ilimin Makarantun Firamare da Sakandare", a Amirka.

Kwanan nan ne, Mis Suemo ta yi bayanai a kan irin abubuwan da ta ƙaru da su, a wani shirin taron 'yan jaridu da Sashen Hulɗa da Jama'a na Ofishin ya shirya a Abuja. Ta ce ziyarar da ta kai Amirka, ba wai kawai ta ba ta damar zagaya makarantu ba ne, da musayar ra'ayoyi da jami'an ilimi na Amirka, har ma ta fahimci hanyoyin da waɗansu ƙasashen duniya ke bi, don bai wa ɗalibansu ingantaccen ilimi. Ta kuma yaba wa irin ilimin da ta samu game da kyawawan hanyoyi da ingantattun manhajoji daban-dabam da ake amfani da su a ƙasashen duniya da tsoma bakin iyaye ga harkokin makarantu, da koyar da ilimi na musamman da kuma yadda ake yin amfani da na'urori na zamani, a kowane fanni na koyar da ilimi.



Mis Ashirshima Suemo (hagu) tare da mataimakin Jami'in Kula da Harkokin Al'adu, Bathelomew Suwa da Jami'in Jaridar "Abuja Inquirer" (dama).

Lokacin da take kamanta harkokin ilimi a Nijeriya da na Amirka, Mis Suemo ta ce, abin da ya fi ba ta sha'awa shi ne yadda ƙungiyoyin sakai na jama'ar Amirka, ke gudanar da harkokin makarantu da kuma matuƙar ƙoƙarin da shugabannin makarantun ke yi, wajen inganta manhajoji, tun daga makarantun firamare.

Ta ce ta sha alwashin hanzarta fara yin amfani da abin da ta koya, a cikin ayyukanta, ta hanyar shirya tarurrukan ƙara wa juna ilimi kan manhajar ilimin firamare da kuma tsoma bakin iyaye, wajen kyautata matsayin makarantun gwamnati da ke yankin na Abuja.

Mis Suemo ta ce, tuni ma har ta fara janyo hankalin abokan aikinta da ke Hukumar Ilimin Firamare, a kan bukatar da ke akwai ta yin amfani da taswirori da sauran kayayyakin koyar da ɗalibai a ɓangayen azuzuwa, kazalika da himmatuwa ga ƙara horar da malamai, don ƙara samun takardun shaida na gaba, don ganin an cimma biyan bukata.

Taron, wanda 'yan jaridu da dama suka halarta, ya haddasa muhawara mai ƙarfi a kan irin halin da harkokin ilimin firamare yake a Nijeriya, a inda 'yan jaridun Nijeriyar da dama suka yi alkawarin yin rubuce-rubuce, a kan ƙalubalen da ke fuskantar ilimin na firamare, da nufin ganin gwamnati ta mayar da shi wani babban al'amari na ƙasa. ■

# Kwallon Kwando Ya Shahara A Nijeriya



Daga hagu: Mohammed Alim Musa, Jami'in Sashen Kula da Wasanni na Hukumar Birnin Tarayya, da ɗan wasa Obinna Ekezie, da Dr. Rudolph E.Stewart, Jami'in Sashen Hulɗa da Jama'a na Ofishin Jakadancin Amirka da kuma Mac Imoni Amarere, mai gabatar da shirin "Kaakaki".

Daga tsakanin 12 zuwa 14 ga watan Agusta, 2005, Sashen Hulɗa da Jama'a na Ofishin Jakadancin Amirka ya tara ɗalibai, maza da mata, daga kowane jinsi, a Cibiyar Wasanni ta Yankin Babban Birnin Tarayya na Abuja, don yin wasanni, musamman ƙwallon kwando.

Wani ɗan Nijeriya ne, shahararre a wasan ƙwallon kwando, Obinna Ekezie tare da Jakadan Amirka, John Campbell, suka bayar da gudunmawar takalman wasa na Reebok ga waɗanda suka shiga wasannin shirin da Ministan Abuja ya ƙaddamar, wanda aka yi wa laƙabin, "Shirin Kawo Zaman Lafiya na Amirka da Hukumar Kwallon Kwando ta Amirka da Kamfanin Kayayyakin Wasa na Reebok da Babban Birnin Tarayya".

Amsa kiran yaran ya yi armashi. Hakika, waɗanda ma suka hallara a sansanin sun wuce yawan da aka yi



Yara da suka hallara a wannan shiri na koyon yadda ake wasan ƙwallon kwando.



Wakilin Ministan Birnin Tarayya na miƙa godiya ga Jakadan Amirka bisa kyautar takalma da kamfanin Reebok ya bayar ta hannun Jakadan.



Shahararren ɗan wasan ƙwallon Kwando, ɗan asalin Nijeriya Obinna Ekezie tare da yara masu sha'awar hazaƙarsa a wannan wasa.

tsammani. Shirin na kwanaki uku, ya haɗa har da jawabi ga 'yan jaridun da ke Birnin Abuja. Dukan idanun 'yan jaridu sai ya koma kan Obinna. An yi hira da shi a gidajen rediyo da telebijin har wani shiri ya halarta a gidan Telebijin na AIT, da ake nunawa da safe, mai suna "Kaakaki". A wajen shirin ya ce "Ina godiya da wannan damar da Amirka ta ba ni, na cimma burina na rayuwa, shi ya sa nake son yara su yi koyi da ni".

Ambasada John Campbell ya ce sansanin wasan na ƙwallon kwando wata alama ce ta irin ƙoƙarin da Cibiyar Wasanni ta Babban Birnin Tarayya da Hukumar Kwallon Kwando ta Amirka da Ofishin Jakadancin Amirka, ke yi. "Muna fata waɗanda suka shiga wannan gasar za su yi amfani da irin abin da muka koyar don yaɗa shi ga yankin babban birnin da kuma sauran jihohi makwabta", in ji shi.

Jami'in da ke wakiltar Ministan na Abuja, Alhaji Sani Lulu Abdullahi, wanda ya karɓi gudunmawar takalman ƙirar Reebok, a madadin Cibiyar Wasan ta Babban Birnin Tarayya, ya nuna cewa Amirka ta gamsu da irin yadda Nijeriya ke bunƙasa wasanni".

Sansanin zaman lafiyar na tarayya, wani haɗin gwiwa ne tsakanin Sashen Bunƙasa Al'adu na Amirka da Kungiyar Kwallon Kwando ta Kasa da Kamfanin Reebok da Cibiyar Wasanni ta Birnin Abuja. Kamfanin Reebok ya bayar da kyautar takalma dubu ɗaya da 500, yayin da Hukumar ECA ta bayar da ƙwallaye 50, duk da yake ita ta ɗauki ɗawainiyar gasar. Cibiyar Wasanni ta Birnin Abuja kuma ta rungumi ɗawainiyar shirya gasar wasan ta kwanaki uku. ■

# Jawabin Jakada Campbell



Ambasada John Campbell tare da Shugaban Hukumar Kula da Wasanni a Birnin Tarayya Abuja, Alhaji Sani Lulu Abdullahi ne suke gaisawa da matasan 'yan wasan ƙwallon kwando.



Obinna Ekezie tare da Jami'an Kungiyar Wasan Kwallon Kwando da na Hukumar Kula da wasanni a Birnin Tarayya, Abuja.

Na san kuna da bukatar ku koma ga wasan ƙwallonku, to zan wuce makaɗi da rawa, a taƙaice in ce, 'yan wasa da manyan baƙi, ina yi muku maraba.

Wannan sansanin na wasan ƙwallon kwando, wata alama ce ta irin ƙoƙarin da Cibiyar Wasanni ta Birnin Abuja, da Kungiyar Wasan Kwallon Kwando ta Kasa da Ofishin Jakadancin Amirka a Nijeriya ke yi, amma ba ta yi tasiri ba, sai da taimakon shahararren ɗan wasan nan, ɗan Nijeriya, Obinna Ekezie.

Wannan sansanin ba zai taɓa ɗorewa ba, in ban da irin ƙoƙarin da jama'a da dama suka yi. Ku taya ni gode wa irin gagarumar gudunmawar da Ofishin Ilimi da Al'adu na Amirka da Kungiyar NBA da Kungiyar Wasan Kwallon Kwando ta Birnin Abuja da Kamfanin Reebok da mai koyar da wasa, Johnson da Kamfanin Louis Berger International da kuma sauran jama'a suka bayar, don ganin samun nasarar wannan shirin.

Ofishin Jakadancin Amirka da Hukumar Wasanni Kwallon Kwando ta Birnin Abuja, suka tara ɗalibai daga kowane jinsi, har 200, don yin wasan ƙwallon kwando, wanda ya zama hanyar lumana da zaman lafiya. Don haka ina mai miƙa godiya ga waɗannan matasan da ke nan yau, domin shiga wannan sansani na wasan ƙwallon kwando.

Ɗaya daga cikin abubuwan sha'awa a wannan sansanin shi ne, takalman wasan ƙwallon kwando fiye da dubu da Kamfanin Reebok ya bayar, domin ƙara wa 'yan wasa ƙwarin gwiwar inganta wasan ƙwallon kwando a Yankin Birnin Abuja. Wannan gudunmawar wani ƙari ne ga takalman da aka bai wa kowane ɗan wasa a sansanin.

Na ji cewa waɗannan takalman wasan ƙwallon kwandon da Kamfanin Reebok ya bayar, wani sabon samfuri ne, na zamani, don haka ina mai alfaharin miƙa su ga Ministan Babban Birnin Abuja,

Malam Nasir El-Rufa'i. Muna godiya ga Kamfanin Reebok. Muna fata irin juriyar da waɗanda suka shiga gasar suka nuna, a lokacin wannan wasan, za ta zama abin koyi ga yankin Birnin Abuja da kuma jihohi maƙwabta.

Kamar kuma mai koyar da wasan, Obinna, wanda ke wasa a Kungiyar Wasan Kwallon Kwando ta Hawks da ke Atlanta, muna kuma fatan Kungiyar NBA, nan gaba, za ta zaƙulo taurari, daga cikin matasan da ke wannan wasan. ■

# Musayar Al'adu Na Inganta Harkokin Shaƙatawa

Shahararrren jarumin nan a fina-finai, kuma wanda ya samu kyautar girmamawa, a fannonin shirin fina-finan Amirka ta Oscar, John Wesley Snipes ya ziyarci Nijeriya, a karo na biyu, a cikin watan Satumba 2005. Jakada John Campbell ya bayyana cewa, maƙasudin wannan ziyarar shi ne don inganta harkokin shaƙatawa a Nijeriya da Amirka ke yi, "wajen yawaita sanin irin yadda al'adun gargajiyar Nijeriya suke". Ya yi ziyararsa ta farko a shekarar 1986.

Lokacin da yake wannan ziyara, Mista Snipes ya buɗe ginin tulluwar harkokin shaƙatawar zamani da ke Babban Birnin Tarayya, Abuja, watau DOME, don zama wani ɓangare na haɓaka harkokin shaƙatawa da saduwa da takwarorinsa da ke fagen harkokin shirye fina-finai na Nijeriya da aka fi sani da suna Nollywood.

Sakatariyar Harkokin Kyautata Jin Daɗin Jama'a na Yankin Babban Birnin Tarayya, Uwargida Bolanle Onagoruwa da Babban Darektan Zauren DOME, Dokta Obiora Okonkwo, sun bayyana cewa wannan ziyarar ta Mista Snipes ta ƙara daraja ga Shirin Inganta Kwarjinin Nijeriya a idanun duniya.

An bai wa Mista Snipes wata sarautar gargajiya da ake kira Mbaukwu, a Jihar Anambra.

An haifi John Wesley Snipes ne ranar 31 ga watan Yuli na 1962, a garin Orlando da ke Florida, ya kuma girma a Kudancin Bronx na Birnin New York. Shi ne kuma wanda ya fi shahara a dukan fina-finan da aka yi na nunin al'adar nan ta matsafan da ke shan jimi, watau Vampire, a cikin sinimansa da ya fito mai suna BLADE, duk da yake dai ya nuna matuƙar hazaƙa, a cikin waɗansu fina-finai daban-dabam.

A 1991 ne, Snipes ya kafa wani kamfanin shirya fina-finai mai zaman kansa da aka fi sani da suna Amen Ra Films. Kamfani na ɗaya daga cikin waɗanda suka shirya ɓangarorin nan biyu na Fin ɗin BLADE da shi Snipe ya zama jarumi a ciki. ■



Jarumin Fina-finai, John Wesley Snipes tare da Jakadan Amirka John Campbell da mai masaukinsa a Nijeriya, Dr. Obiora Okonkwo (hagu).



Jami'in Sashen Hulɗa da Jama'a, Dr. Rudolph E.. Stewart ne yake jawabi game da ayyukan da aka shirya na maraba ga wannan babban baƙo. Ta biyu a zaune daga dama ita ce Wakiliyar Hukumar Birnin tarayya a wannan taro, watau Mis Bolonle Onagoruwa.

# Hukukmar Bunƙasa Ciniki Ta Amirka Ta Goyi Bayan Sake Tsarin Harkokin Iskar Gas Ta Nijeriya



Musabaha da karɓar takardar wannan yarjejeniyar tsakannin ƙasar Amirka da Nijeriya.

Hukumar Bunƙasa Harkokin Ciniki ta Amirka (TDA) ta bai wa Nijeriya dalar Amirka dubu 562, ta hannun ofishin Karamin Ministan Harkokin Man Fetur, domin taimaka wa harkokin fasahar sake tsari da ɓullo da dabarun tanadin albarkatun iskar gas (LPG). An tabbar da karɓar wannan kuɗin ne, a wani bikin sanya hannu da aka yi, a ofishin ministan a Babban Ofishin Hukumar Harkokin Man Fetur na Nijeriya.

Jakadan Amirka, John Campbell da Ministan, Dokta Edmund Daukuro ne suka sanya hannu a madadin ƙasashensu, Amirka da Nijeriya.

Ministan Harkokin Man Fetur na Nijeriya, Dokta Edmund Daukuro, ya bayyana a wajen bikin sanya hannun cewa, kuɗin na TDA, wani babban yunƙuri ne, muhimmi, wanda ya yi daidai da irin tsarin da ƙasar nan ta yi, na bunƙasa harkokin samar da makamashi.

Ya ce a shekarun da suka wuce, irin yawan iskar gas da ake amfani da ita a cikin gida ya ragu daga fiye da ton dubu 100, a farkon shekarar 1980 ya zuwa ton dubu 54 a cikin 2004.

Idan aka duba irin yawan jama'a kuma zai nuna cewa kowane ɗan ƙasa yana amfani da ƙasa da kilo ɗaya na iskar ta gas, wanda kuma shi ne mafi ƙanƙanta a duk yankin Afirka, wanda ya nuna "idan ba a yi sannu ba, to masana'antar za ta durƙushe", in ji shi.

Ya jaddada cewa, duk waɗansu bukatun da ake da su, dangane da dabarun kyautata harkokin sassan aikin hukumar ta iskar gas (LPG), kamar yadda Ambasada Campbell ya bayyana, a matsayin "haɗin gwiwa na zahiri da zai bayar da damar sake farfaɗo da kasuwar iskar gas ne domin dafe-dafe".

Ambasada Campbell ya ce, "tattali da magance haɗarin iskar ta gas wani abu ne da ya damu harkokin rayuwar kowane ɗan Nijeriya. Amma iskar ta gas ba ta kai wa ga talakan Nijeriya, wanda abin da wannan haɗin gwiwar ke son ya gyara".

Za a yi amfani da taimakon na TDA don wadata Nijeriya da miƙaƙƙiyar hanya, mafi inganci, ta sake fasalin kasuwar Hukumar ta LPG. Shirin taimakon na TDA, musamman zai ƙunshi yin gyara da kwaskwarimar farashinsa, kazalika da sanin yadda za a riƙa bi don farfaɗo da kasuwarsa, da nufin janyo hankalin masu zuba jari, yayin da za a ci gaba da tanadin gyare-gyaren da aka yi.

Hukumar Bunƙasa Harkokin Ciniki ta Amirka ce, ke taimako ga kawo ci gaban bunƙasar tattalin arziki da sha'awar harkokin cinikayya da Amirka, a ƙasashe masu tasowa da ƙasashe masu matsakaicin arziki.



Jami'an Ma'aikatar Harkokin Man Fetur tare da babbar sakatariyar wannan Ma'aikata, Hajiya Ammuna Lawan-Ali da Babban Darakatan kamfannin NNPC, Injiniya Funsho Kupolokun da wasu attajirai masu harkokin mai da iskar gas.

Hukumar na bayar da kuɗaɗe ta fannonin harkokin fasaha da nazarin share fage, da harkokin horaswa da kai ziyarce-ziyarce da kuma tarurrukan harkokin ciniki, waɗanda ke mara wa inganta kayayyakin zamani da samun sararin buɗe kasuwannin duniya.

Dabarun Shirin na TDA, na taimaka wa ƙasashen duniya da ƙwaƙƙwaran hanyar tafiyar da jari, da gudanar da ra'ayoyin ƙasashen da aka bai wa kuɗin, don ganin sun samu ci gaban ciniki da zuba jari ga tattalin arzikinsu.

Maƙasudi kuma shi ne don ganin an kai ga biyan bukatar ɓangaren tattalin arzikin Amirka ta fannin saye da sayar da kayayyakin Amirka, a ƙasashen waje. ■



Daga hagu: Shannon M. Ross, Jami'ar Sashen Wutar lantarki da Makamashi, da Ambasada John Campbell da kuma Dokta Edmond Dakoru, Minista a Ma'aikatar Harkokin Man Fetur.

# Amirka Ta Goyi Bayan Bincike A Kan Sabuwar Hanyar Warkar da Cutar Kanjamau

## Tashin farko game da sabuwar hanyar kai hari ga ƙwayoyin cutar ƙanjamau

Bincike da Gwamnatin Amirka ta ɗauki ɗawainiyar gudanarwa, ya buɗe ƙofar bin sabuwar dabarar binciken da ke iya kaiwa ga gano maganin cutar ƙanjamau da kawar da ƙwayoyin cutar, a jikin jama'a, kamar yadda aka bayar da rahoton daga Jami'ar Arewacin Carolina da ke Chapel Hill (UNC).

Masu bincike sun yi amfani da wani maganin da bai dankwafarwa, don kai hari ga ƙwayoyin cutar ƙanjamau da ke laɓewa a cikin waɗansu halittun, yadda ƙwayoyin magani na HAART ba su iya kashe su. Wannan maganin ya yi tasiri, wajen kai hari ga ƙwayoyin cutar ƙanjamau da ke laɓewa, ya sa a riƙa samun sauƙi, amma ba maganin ba.


Binciken, wanda aka buga a Mujallar Lancet, a ranar 13 ga watan Agusta, ya gano cewa, ɗiga ƙarin maganin Valproate ga magungunan da ake bai wa mai cutar ƙanjamau, yana kai hari ga ƙwayoyin cutar ƙanjamau da ke laɓewa, ya wargaza halittar da ke sa ƙwayoyin suna kwanton ɓauna.

Binciken ya gano cewa maganin na dankwafe kashi 75 cikin 100, na kwanton ɓaunar da cutar ke yi, lokacin da ake gwaji har sau huɗu, a kan al'amarin.

"Bincikenmu ya bayar da shawara a kan wata sabuwar hanyar fuskantar kashe kamuwa da cutar ƙanjamau, har ya zuwa cikin halittun da suke laɓewa," in ji babban mawallafin rahoton, kuma farfesan harkokin magani da binciken ƙananan halittu da magungunan rigakafi, na Kolejin Likitoci da Jami'ar UNC, Dokta David M. Margolis.


Margolis na cikin ƙungiyar Cibiyar Harkokin Likita ta Kudu maso Yammaci, da ke Jami'ar Texas, ta Dallas, lokacin da aka gudanar da binciken.

Cibiyar Nazarin Harkokin Kiwon Lafiyar Jama'a da Harkokin Binciken Cututtukan Dabbobi suka tallafa wa binciken. ■



Hoton ƙwayoyin jini da ke kare mutun daga kamuwa da cututtuka, wanda a nan ƙwayoyin HIV sun harbe su, sun kuma lalata su.

©Museum of Science and Industry, Chicago.



Kwayar HIV mai karya garkuwar jiki.

©Avert

# Ana Iya Rage Karancin Rashin Koshin Yara A Afirka Nan Da 2015 - *In ji wani Rahoto*

## *Bincike ya ce ana iya cimma nasara, in aka sake fasalin ra'ayoyi da zuba jari.*

Daga Aviva Altmann
*daga Birnin Washington*

Duk da irin hauhawar da rashin abinci mai gina jiki ke yi a Afirka, a cikin fiye da shekaru 30 da suka wuce, wani rahoto ya bayyana cewa, muddin aka sake fasalin aiwatar da ra'ayoyi da zuba jari, to yaran Afirka fiye da rabi za su riƙa samun abinci mai gina jiki, nan da 2015.

Ranar 11 ga watan Agusta ne, Cibiyar Bincike A Kan Ra'ayoyin Abinci Ta Duniya (IFPRI), ta bayar da wani rahoto mai laƙabi "Hangen Nesan Bunƙasa Harkokin Noma da Tanadin Abinci A Afirka", ga gidajen watsa labarai da ke Amirka da Ingila da kuma Afirka.

Wannan ba rahoton soki-burutsu ba ne", in ji Shugaban Cibiyar ta IFPRI, dangane da Hasashe A Kan Noma, Abinci Da Muhalli, nan da 2020, Rajul Pandya-Lorch. "Idan aka samar da isasshen jari, to za a rage yawan yaran Afirka, da ba su samun isasshen abinci mai gina jiki, ya zuwa rabi".

Rahoton ya nuna cewa, muddin kuma al'amarin aiwatar da ra'ayoyin da zuba jarin ya ɗore (abin da IFPRI ta kira "kasuwar Allah ya amfana"), to yawan yaran Afirka da za su rasa abinci zai ƙaru da kusan miliyan 3 da dubu 300, nan da zuwa 2025.

Idan kuma aka samu koma-bayan harkokin jarin cikin gida da ƙasashen waje, Hukumar IFPRI tana sa ran abin da ta kira "halin ha'ula'in" da za a samu yaran yankin Saharar Afirka da za su rasa abinci mai gina jiki, har miliyan 55 da dubu 100, a cikin 2025 kaɗai, wanda yake ƙaruwa da fiye da yara miliyan 22 da dubu 100 tun cikin 1997.





Yara da ke fama da ciwon rashin abinci mai gina jiki.

©Francis Temman/AP
Finbarr O;Reily/Reuters

Amma rahoton ya ɓullo da wani abin da Hukumar IFPRI ta kira "jagora", wanda ya lura cewa dole a riƙa bincika manufar Bukatar Cimma Burin Wannan Karnin, na rage yawan mutanen da ke fama da yunwa, ya zuwa rabi, a 2015. Muddin kuma aka yi aiki da wannan manufa, yadda ya kamata, rahoton ya yi ƙiyasin cewa, lalle za a iya rage yawan yaran da ke fama da rashin abinci mai gina jiki, da rabi, da miliyan 15 da dubu 100, nan da 2015, a kuma ƙara rage yawansu da miliyan 9 da dubu 400 a cikin 2025.

Daraktan Kula da Muhalli da Inganta Harkokin Fasaha, na Hukumar ta IFPRI, wanda kuma shi ne mawallafin rahoton, Mark Rosegrant, ya yi bayani a kan irin canjin da ya kamata a yi, don cimma nasarar shirin.

"Bincikenmu ya nuna cewa, tuni ake da bukatar zuba ƙarin jarin dalar Amirka miliyan dubu 4 da 700, a kowace shekara a kan yawan jarin da aka zuba wa "kasuwar Allah ya amfana".

Da canjin aiwatar da ra'ayoyin da za su ƙalubalanci rashin abinci mai gina jikin da yaran Afirka da sauran ƙasashen da suka samu ci gaba, a duniya ke bukata, in ji Rosegrant.

Duba Shafi Na 19

# USAID Da Nijeriya Sun Duƙufa A Kan Rage Rashin Abinci Mai Gina Jiki Ga Yaran 'Yan Kasa Da Shekaru Biyar

Shirin Haɗin Gwiwar Ceto Yara na Hukumar USAID da Nijeriya, Rukuni na Biyu, ya ɓullo da Kwaƙƙwaran Shirin Kiwon Lafiya (PD/Health), a waɗansu yankunan ƙananan Hukumomin Jihar Kano, a 2003.

Har yanzu kuma ana ta amfana da shirin, yayin da kwanan nan za a faɗaɗa shi zuwa waɗansu jihohi huɗu, ta hannun shirin haɗin gwiwar wadata harkokin kyautata jin daɗin rayuwa, COMPASS.

Da farko an ɓullo da shirin na PD/Health ne, domin hanzarta tayar da komaɗar ƙanjamammun yara, wanda kuma a cikin makonni biyu kacal sai ga shi an samu nasara, ya kuma yi matuƙar fa'ida ga taimaka wa iyaye mata ga sanin irin abubuwan da iyalai ke bukata, don magance rashin abinci mai gina jiki.

· Hukumar USAID ta iza da bayar da kuɗin gudanar da Safiyon Sanin Yawan Abinci Mai Gina Jiki Na Kasa, da Nijeriya ke bukata a cikin shekaru 30. An kuma bayar da rahoton binciken a 2003, wanda da shi dukan hukumomin ƙasar nan ke amfani, wajen shirya waɗansu ayyukan samar da abinci mai gina jiki.

· Hukumar USAID ce ta fara Shirin Makon Tunawa da Lafiyar Yara, a Nijeriya, sau biyu a shekara, don bincika lafiyar yara da nufin inganta dukan abin da ya shafi lafiyar yara 'yan ƙasa da shekaru biyar, da wadata sinadarin vitamin A, da koyar da yadda ake haɗa kayayyakin




©WFP Markus Prior
Schalk Van Zuyydan/AP

Mata da yara ƙanana na bukantar abinci mai sinadarin gina jiki da samar da koshin lafiya.

abinci mai gina jiki da bayar da maganin tsutsar ciki da ke hana wa yara samun isasshen abinci mai gina jiki.

Yanzu ma, Shirin Haɗin Gwiwar Kungiyoyin Samar da Abinci Mai Gina Jiki, da gwamnatin Nijeriya, na ƙoƙarin game dukan faɗin ƙasar nan.

· Hukumar ta USAID, yanzu tana gudanar da ayyukanta tare da Shirin na gwamnatin Nijeriya, a ƙarƙashin shugabancin Daraktan Noma da Masana'antu na Hukumar Tsara Al'amurran Kasa.

Sauran kuma su ne dukan ƙungiyoyin da ke bayar da agajin abubuwan gina jiki, ga ma'aikatu da hukumomin da ke kula da abinci mai gina jiki da kare lafiyar abinci da kamfanoni da ƙungiyoyi masu zaman kansu, da makarantu da ƙungiyoyi kamar Kungiyar Abinci Mai Gina Jiki ta Kasa da IITA da NEPAD. Shirin ne ya kafa Babban Ofishin Kwamitin Kasa a kan Abinci da Abubuwan Gina Jiki, NCFN, wanda shi ne tushen farfaɗo da kwamitin da ƙaddamarwar da shugaban ƙasa ya yi ta Shirin Manufar Wadata Abinci Mai Gina Jiki ta Kasa, wata hanyar da za a daɗe ana cin gajiyarta a ƙasar nan, saboda manufarta da kuma irin yadda hukumomi da ƙungiyoyi da dama suka haɗe wuri guda, don tabbatar da ganin an aiwatar da duk wani shirin da wannan manufar ta tanada. Wannan shirin ya kai gaya ga samun biyan bukata da kuma binciko duk wata illa da rashin abinci mai gina jiki da yunwar da ke addabar jama'ar Nijeriya.

· A halin yanzu Hukumar USAID, tare da haɗin gwiwar COMPASS, na mayar da hankali ga ƙananan hukumomi 51, a jihohi 5, don inganta sha'anin bai wa jarirai nonon uwa, aƙalla watanni shida, na rayuwarsa, da kuma waɗansu hanyoyin shayar da jariri daga haihuwa zuwa watanni shida.

Da shirin shayar da jariri nonon uwa, har zuwa shekaru biyu, da inganta amfani da sinadarin vitamin A, ya-Allah ta hanyar allurar rigakafi, ko ta shirye-shiryen da aka

saba, kamar Makon Tunawa da Lafiyar Yara da wuraren shan magani, da nuna wa iyaye mata hanyoyin da suka kamata da kuma aiwatar da shirin PD/Health.

Hukumar USAID ce ke jagora da bayar da ƙwararan shawarwarin shirin nan na PROFILES, wata hanyar da dukan gwamnatoci ke amfani da ita, ko da yaushe, ta hannun ƙungiyoyin jama'a, don faɗakarwa game da munanan illolin da rashin abinci mai gina jiki ke haddasa wa ga harkokin rayuwa, da tattalin arziki da kuma na siyasa a ƙasar nan.

Dole kuma a ci gaba da sake bincikar tsarin shirin, saboda yanayin yau da kullum, musamman ganin ya yi tasiri, don bayar da hujja ga shugabanni da ƙungiyoyin da ke tallafawa da kuɗin da ake gudanar da ayyukan da suka shafi wadata abubuwa na gina jiki da kiyaye ingancin abinci.

Dukanmu muna da laifi. Amma mummunan laifinmu shi ne barin yara babu tarbiyya. Wannan shi ne banzatar da tushen duk wata rayuwa.

Abubuwa da dama da muke kai wa hari ba su da wata fa'ida ga rayuwarmu. Amma yara fa?

Yanzu ne ya kamata mu kula da tarbiyyarsu, ko kuma "gobe" ba mu da wani bakin Magana……

- in ji Gabriela Mistral

Yau ne ya kamata!!! ■

# Ana Iya Rage Karancin Rashin Koshin Yara

Daga Shafi Na 17

Rahoton ya bayar da shawarwarin inganta tanadin abinci.

Don kuma ganin an bayar da gudunmawar da ake bukata game da tanadin abinci da kyautata muhalli, Hukumar IFPRI ta bayar da shawarar zuba jari ga noman rani, a ƙara yawan ya zuwa kashi 141 cikin 100, na dalar Amirka miliyan dubu 48 da 700.

Ruwan sha kuma a inganta shi da kashi 55 cikin 100 na jimlar kuɗi dalar Amirka miliyan dubu 49 da 100.

Bukatar ruwan sha a Afirka kullum ƙaruwa take yi matuƙa. Ana sa ran bukatar za ta ƙaru da kashi 67 cikin 100 nan da shekaru 20.

Rahoton ya nuna cewa da zarar damina ta sauka sosai, to babu sauran fari. "Idan kuma aka samu isasshen ruwa, a yankunan da ke da faƙo a Afirka, to za a samu ƙarin albarkar noma, kuma farashi zai sauka, idan kuma aka himmatu ga aikin noman rani, to za a magance hauhawar farashi", a cewar taƙaitaccen rahoton na Hukumar IFPRI.

Rahoton ya yi hasashen a yankin Saharar Afirka kaɗai, ana iya rage yawan tsabar da ake sayowa, ya zuwa rabi, daga ton miliyan 17 da dubu 400 a kowace shekara, ya zuwa ton miliyan 8 da dubu 700, kowace shekara, tsakanin 2021-25.

Ana sa ran za a iya ƙara tanadin yawan kayan abinci, muddin aka inganta harkokin ilimi, musamman na ƙananan mata ko da yake ba shi da alaƙa kai-tsaye da noma.

Rahoton ya yi kira da a ƙara yawan kuɗin inganta kayayyakin aikin ya zuwa dalar Amirka miliyan dubu 95 da 400, da kuma kashi 117 cikin 100 na yawan kuɗin da ake bai wa harkokin ilimi ya zuwa jimlar dalar Amirka miliyan dubu 82 da 300.

> **Bukatar ruwan sha a Afirka kullum ƙaruwa take yi matuƙa. Ana sa ran bukatar za ta ƙaru da kashi 67 cikin 100 nan da shekaru 20.**

An hango ƙaruwar ingancin aiwatar da ra'ayoyi, da harkokin kasuwanci da na sadarwa, da za su rage yawan rashin abinci mai gina jiki a Afirka, su kuma rage yawan irin wahalolin da ake sha ga aikin noma.

Rahoton ya yi jagorancin masu faɗa a ji, a Afirka da ƙungiyoyin da ke bayar da agaji na duniya, kamar yadda aka tsara, da su taimaka ga yin kwaskwarima ga manufofin Taron Millenium+5, a Birnin New York, game da Cimma Biyan Bukata a Wannan Karnin.

"Idan ƙasashen da ke Majalisar Ɗinkin Duniya, suka yi taron 14 ga watan Satumba, suna da damar yin gyara a kan alkawurransu na shekaru biyar da suka wuce.

Muddin da gaske suke yi, game da cika alkawurran, to suna bukatar bayar da himma wajen kawo canji a Afirka, in ji Rosegrant. ■

## Wasiƙu

Cigaba daga inda aka kwana

Waɗanda suke wannan ta'addanci inda Yahudun Isra'ila suka kashe mata da yara da tsoffi 'yan Palasɗinu da rusa masu gidaje, sai Amirka ta gode, ta ce ya yi kyau, ai suna kare kai ne, amma su ba ta'addanci suke ba. Kuma ba 'yan ta'adda ba ne. Saboda haka, ya kamata duk wanda ya yi laifi irin na su Osama bin Laden da Sharon a kira su yan ta'adda, kuma sun yi ta'addanci.

Ya kamata Amirka ta sa Isra'ila ta fice daga ƙasar Palasɗinu a ba su ƙasarsu. Duk duniya Amirka ce kadai za ta iya tabbatar da zaman lafiya a Gabas Ta Tsakiya amma tana numa son kai; A ƙasashen Larabawa, ta ce ya yi daidai kare kai ne, amma a ƙasashen Yahudawa ta ce ta'addanci ne. Ya kamata ta gyara siyasarta ta harkokin ƙasashen waje. Ta daina nuna son kai.

Duk wanda ya yi laifi ta ce ya yi, kuma ta daina matsa wa ƙasashen Larabawa don maganar makaman nukiliya ai Isra'ila na da shi. Ba ta yi magana a kanta ba alhali, Isra'ila barazana ce ga ƙasashen Larabawa . Ya kamata a rushe kowaccensu ko a ba kowaccensu dama ta mallaka. Kuma Amirka ta tilasta wa sojojinta da sake yaƙi ƙasashen Larabawa su girmama al'ada da addinin mutanen ƙasashen. Domin ba mu ji dadin labarin yadda sojojin Amirka suka wulakanta Alƙur'ani Mai Girma a Kurkukun Guatanamo. Wannan abu ya tozartar da Musulmai.

Ya kamata a girmama mutane da addininsu da kuma dukkan littafan addininsu kuma ta fice daga ƙasashen Musulmi, ta rage shiga sharo ba shanu.


Wanda ya aikata aiki gwargadono sharri ko hairan zai gani.

Haruna Tilde

Kaduna.

Za'a ka iya aiko mana da wasiƙu ta hanyar e-mail a wannan adireshi: magama@state.gov

*Kuma zaku iya karanta mujallarmu a intanet. Don haka, ku aiko mana da adireshin ku na e-mail a wannan adireshi: magama-ng@lists.state.gov domin mu rika aiko muku da mujallarmu kai tsaye a duk lokacin da muka fito.*




## RA'AYINKA

Idan ka samu mujallar *Magama,* muna bukatar ra'ayinka game da ita.

Suna ..................................................

.........................................................

Adireshi na e-mail.............................

.........................................................

.........................................................

Yaya kake bukatar mu riƙa aiko maka da mujallar *Magama?*............................

..........................................................

*Ka aiko mana da dukan bayanai ta hanyar e-mail ko kuma akwatin gidan waya mai lamba: 5760 Garki, Abuja.*

e-mail zuwa ga edita: magama@state.gov

# Ziyarar Shahararren Jarumin Fina-finai John Wesley Snipes.



Daga dama: Maxine A. Hanks, da Cristina Marko, da kuma Dr. Rudolph E. Stewart.



Jami'an Ofishin Jakadancin Amirka da ke Abuja tare da sauran baƙi ne suke taɗi da babban baƙon.



Shahararren Jarumin Fina-finai, John Wesley Snipes ya ziyarci Ofishin Jakadancin Amirka da ke Abuja tare da mai masaukinsa Dr. Obiora Okonkwo, babban Daraktan Kulob ɗin nan mai Laƙabin DOME.




Daga dama: Uwargida Bolanle Onagoruwa, da Ambasada John Campbell, da Dr. Obiora Okonkwo, sai kuma John Wesley Snipes.



John Wesley Snipes ne yake sa hannu a littafi a matsayinsa na babban baƙo a gidan Jakadan Amirka da ke Abuja.

# Koyi Da Gwani Jari

Shahararren ɗan wasan Kwallon Kwando, Ɗan asalin Nijeriya da ke wasa a Amirka, Obinna Ekezie, na koya wa matasan Nijeriya yadda za su ci gajiyar Kwallon Kwando.




## Satumba 2005

| Sun | Mon | Tue | Wed | Thu | Fri | Sat |
|---|---|---|---|---|---|---|
| | | | | 1<br>Ganawa da 'yan jaridu a Abuja | 2 | 3 |
| 4 | 5 | 6 | 7<br>Sabon Shugaban [akin karatu, Henry Neil Mendlesohn zai iso Abuja<br>Ziyarar Shahararren Jarumin Fina-Finai John Wesley Snipes | 8<br>Ganawa da 'yan jaridu a Abuja<br>Ziyarar Shahararren Jarumin Fina-Finai John Wesley Snipes | 9<br>Tafiyar Mis Hauwa Abubakar zuwa Amirka dom in shiga bitar hanyoyin tattalin arzikin mata<br>Ziyarar Shahararren Jarumin Fina-Finai John Wesley Snipes | 10<br>Ziyarar Shahararren Jarumin Fina-Finai John Wesley Snipes<br>Ziyarar Tsohon Shugaban Amirka Jimmy Carter da Uwargidansa Rosalynn |
| 11<br>Ziyarar Shahararren Jarumin Fina-Finai John Wesley Snipes<br>Ziyarar Tsohon Shugaban Amirka Jimmy Carter da Uwargidansa Rosalynn | 12<br>Ziyarar Shahararren Jarumin Fina-Finai John Wesley Snipes<br>Ziyarar Tsohon Shugaban Amirka Jimmy Carter da Uwargidansa Rosalynn | 13<br>Ziyarar Shahararren Jarumin Fina-Finai John Wesley Snipes<br>Ziyarar Tsohon Shugaban Amirka Jimmy Carter da Uwargidansa Rosalynn | 14<br>Ziyarar Shahararren Jarumin Fina-Finai John Wesley Snipes | 15<br>Ganawa da 'yan jaridu a Abuja | 16 | 17 |
| 18 | 19 | 20<br>Mis Maren Milligan, [aliba a harkokin mulki da siyasa a Jami'ar Maryland zata fara ayyukanta a Jami'ar Bayero na bincikenhalinrayuwa dahanyoyin inganta zaman lafiya a cikin al'umma a karkashin Shirin Fulbright | 21<br>Za~en wakilan Nijeriya a shirin Fulbright da Humphrey | 22<br>Ganawa da 'yan jaridu a Abuja | 23 | 24 |
| 25 | 26 | 27 | 28 | 29<br>Ganawa da 'yan jaridu a Abuja | 30 | |

Wallafar Ofishin Jakadancin Amirka, Nijeriya